# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Cin zarafi ta hanyar lalata tsa kanin al’umma a Afirka
## Kashi na huɗu: Alamun janyewa

Wanda ya rubuta: Chrispin Mwakideu
Wanda ya fassara: Yusuf Idris
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**’Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Jammo: | ɗan shekara 45 |
| Adams: | ɗan shekara 10 |
| Hadiza: | ’yar shekara 30 |
| Dauda: | ɗan shekara 40 |
| Likita: | ɗan shekara 50 |
| Fati: | ’yar shekara 16 |
| Sherifat: | ’yar shekara 40 |
| Precious: | ’yar shekara 30 |

**Mai gabatarwa:**

Masu sauraronmu, barkanmu da sake saduwa da ku a cikin wannan sabon shiri na "Ji Ka Karu" wanda yake zuwa muku daga nan kafar rediyo ta Deutsche Welle da ke nan birnin Bonn, a kan cin zarafi da wulaƙanta 'ya'ya mata a ƙasashen Afirka. Muna cikin kashi na huɗu a cikin jerin shirye-shiryen da muke kawo muku a kan wannan batu. A cikin shirin da ya gabata kun ji yadda Dauda ya gaggauta kai matarsa asibiti bayan halin da ta samu kanta a ciki a bakin kogi. A babbar makarantar Mai Aduwa kuma, Malam Tanko ya ci zarafin 'yar ƙaramar yarinya Fati duk da cewa shi malaminta ne.

Sai ku kasance da mu a cikin wannan shiri mai taken "Abin da ya biyo baya". Za mu faro ne daga gidan su Adams, yaron nan ɗan shekaru goma da haihuwa. Yamma ta yi sosai, kuma mahaifiyar Adams ta tafi aiki, ta bar shi a hannun kulawar sabon sarauyinta, wato Jammo.

**Fitowa ta 1: A gidan su Adams**

**Jammo:** Adams! Me na ce maka a kan buɗe rediyo yana ƙara haka? Adams! Ba da kai nake magana ba?! Me na taɓa ce maka a kan buɗe rediyo yana ƙara haka? Na ce ka rage ƙarar rediyon nan! Maƙwabtanmu ba sa son jin irin waƙar da kake sawa. Na ce ka rage ƙarar rediyon nan yanzun nan! … To, tun da yau ka son yin magana, maza ka tashi ka je ka yi wanka, sannan ka tafi ka kwanta. Ka ji ko? Na ce ka ji ni ko?

**Adams:** Eee.

**Jammo:** Oho, ya yi kyau, ashe kana iya yin magana. Maza ka tafi, ka kuma tabbatar da cewa ka wanke kanka da kyau.

**Mai ba da labari:**

Adams yana cikin wani hali na tsoro. Bai taɓa haɗuwa da wani mugun mutum ba a rayuwarshi kamar mutumin da mahaifiyarshi ta kawo. Amma kash, Adams zai gane cewa dukan da Kawu Jammo ya yi mai ƙaramin al'amari ne a kan abin da zai ƙara biyo baya. Adams dai ya yi abin da aka ce ya yi, wato ya je ya yi wanka.

**Jammo:** Yauwa, su Adams manya!

**Adams:** Kawu Jammo! Ka fita daga nan! Ba ka ganin wanka nake yi! .,.. a'a, kawu Jammo… me..me kake yi haka?

**Jammo:** Kai, saurara mana! Zo, zo!

**Adams:** Aaa, Kawu Jammo! Aaaaaa…..!

**Jammo:** Kai, kar ka rufe min asiri, ka yi shiru!

**Mai ba da labari:**

Ga yawancin jama'ar Afirka, yin jima'i ba ta halatacciyar hanya ba ya haramta. Saboda haka ba kasafai ake maganarshi ba. Iyaye maza ba sa iya yi wa 'ya'yansu maza maganar, ballantana iyaye mata. Saboda haka ba abin mamaki ba ne a ji cewa ba a tattauna wani abu da ya shafi cin zarafi, ko fyaɗe a yawancin gidajen 'yan Afirka ba. Ga yawancin mutane ma, ba su yarda da cewa wannan abu yana faruwa ba har sai ya faru a kansu. Kawu Jammo yana amfani da irin wannan tunanin da kuma ƙanƙantar yaron nan Adams don cin zarafinsa. An danƙa amanar ɗan ƙaramin yaro a hannunshi, amma maimakon ya kula da shi sai ya ci zarafinshi. Yanzu me zai faru? Nan ba da daɗewa ba za mu ji.

A wani ɓangare na ƙasar kuma Hadiza tana asibiti bayan mummunan halin da ta shiga na fyaɗe. Ta ɗan daɗe a some, amma san da ta farfaɗo mijinta

Dauda na zaune a gefen gadonta.

**Fitowa ta 2: A asibiti**

**Dauda:** Kai! Hadiza, abar ƙaunata. Na ji daɗin ganin cewa kin farfaɗo. Sannu, kin ji.

**Hadiza:** Dauda, me ya faru? Me ya kawo ni asibiti? Wayyo Allahna! Don Allah ka ce min ba gaskiya ba ne. Ba na son in tuna da duk abin da ya faru!

**Dauda:** Ki daina kuka, Hadiza. Ki kwantar da hankalin ki! Yanzu kina tare da ni, ba wani abu. Don Allah Hadiza, ki daina kuka.

**Likita:** Yauwa, ai ina ganin komai ya yi daidai tun da ga shi Hadiza ta farka. Da ma akwai labarin da nake so ku ji dukkanku gaba ɗaya.

**Dauda:** Dokta, labarin ba zai iya jira ba har zuwa wani lokaci?

**Likita:** A'a, haƙuri za ka yi. Ka yi haƙuri, ba zan iya jira ba har sai wani lokaci. Hadiza, a matsayina na likita, abu mafi wahala a wajena ba warkar da jama'a ba ne idan ba su da lafiya, sai dai ba da labari irin wannan.

**Hadiza:** Me ya faru, Likita? Zan mutu ne? Labarin ke nan?

**Likita:** Hadiza, ki kwantar da hankalinki! Ya yi kyau da aka kawo ki asibitin da wuri, sai dai kuma abin takaici …

**Dauda:** Likita, kar dai a ce sun sa mata cutar HIV!

**Likita:** Dauda, ka yi haƙuri ka saurare ni. Na san cewa wannan wani lokaci ne mai wuyan gaske a wajenku. Amma a matsayina na likita kamar yadda na ce ne, ya yi kyau da aka kawo ki asibiti a kan lokaci. Haka zai ba mu damar duba raunukan da kika ji da kyau. Sai dai saboda mummunun cin zarafin da aka yi miki kin samu ɓarin cikinki.

**Dauda:** Mene! Wayyo Allahna! Me yake faruwa haka?

**Hadiza:** Ka yi haƙuri Dauda, na yi ƙoƙari. Na yi duk iyakacin ƙoƙarina, amma suna da yawa kuma sun fi ƙarfina.

**Likita:** Yi haƙuri, yi haƙuri! Na san cewa wannan mawuyacin hali ne a gare ku. Sai mu gode wa Allah cewa Hadiza tana da ranta bayan duk abin da ya same ta. Za mu yi gwajin HIV bayan watanni uku da aukuwar wannan abin. Kuma za mu yi iyakar ƙoƙarinmu don mu ga cewa kin sami lafiya sosai.

**Dauda:** Kai! 'Yarmu… yarinyarmu...

**Hadiza:** Dauda, don Allah kar ka yi fushi da ni! Ba laifina ba ne!

**Dauda:** Me ya sa haka zai faru da mu? Me ya sa zai faru da ni? Me ya sa zai faru yanzu? Kaiiii! Sai na kashe dabbobin da suka yi mini wannan munin abin!

**Likita:** Yallaɓai, matarka ta shiga wani mawuyacin hali na cin zarafi da tashin hankali. Za mu yi iyakacin ƙoƙarinmu a wannan asibitin don mu ga mun warkar da cututtukan da ta samu. Amma yana da muhimmancin gaske a nemi taimako ta yadda abin ba zai zauna a zuciyarta ba. Idan

har kana son wannan, to sai ta nemi taimakon wanda ya ƙware a kan ba da shawarwari ta wannan hanyar. Amma yallaɓai, abin da matarka ta fi buƙata a yanzu shi ne kai, kai kanka! Ɓa wani abu da irin jama'ar da wannan abin ya shafa ke buƙata illa ƙauna daga waɗanda suka fi yarda da su!

**Dauda:** Hadiza, abar ƙaunata, kar ki damu! Ka yi haƙuri, Likita, abin ne ya tayar min da hankali sosai. Hadiza ta shiga cikin wani mawuyacin hali, sannan kuma yanzu a ce wannan abin ya faru. Amma ba wani abu, Hadiza, ba wani abu. Ki yi barci. Sai gobe da safe in Allah ya yarda zan zo.

**Hadiza:** Dauda, na gode wa Allah da ya ba ni kai a matsayin miji. Ba don kai ba, da na mutu.

**Mai ba da labari:**

Dole ne Hadiza ta rungumi ƙaddara saboda halin da ta samu kanta a ciki. Amma yanzu bari mu koma wajen Fati wadda ta je gida a ƙarshen mako domin ziyartar mahaifiyarta Sherifat. Yanzu dai hantsi ya fito sosai amma har yanzu Fati na kwance a kan gado.

**Fitowa ta 3: A gidan su Fati**

**Sherifat:** Fati! Fati! … Fatiiiii!

**Fati:** Na'aaam…

**Sherifat:** Ina fata dai ba irin wannan barcin kike yi a makaranta ba. Ikon Allah! Har ƙarfe goma fa ta kusan yi! Me ya same ki haka? Kin daina zuwa irin gudun safen da kike yi ne?

**Fati:** Mama, don Allah ki yi haƙuri ki ƙyale ni in ɗan ƙara yin barci, na gaji.

**Sherifat:** Kin gaji? Shekarunki goma sha shida amma kina yin abu sai ka ce wadda ta kai shekaru sittin. Don Allah ki tashi! Ki zo ki taya ni share-share. Za mu yi baƙi an jima.

**Fati:** Ni ba na son ganin kowa.

**Sherifat:** Fati! Me kika ce?

**Fati:** Mama, don Allah ki ƙyale ni. Ki tuna lokacin da kika kai ni makaranta. Kin ce ya kamata a ce ina da dama na ɗan kasance ni kaɗai. To yanzu ina buƙatar in kasance ni kaɗai.

**Sherifat:** A'a… To shi ke nan, idan haka kike so. Amma dai ba wani abin da yake damunki ko?

**Fati:** A'a.

**Sherifat:** Lafiyarki ƙalau?

**Fati:** E.

**Sherifat:** Makaranta lafiya lau?

**Fati:** Don Allah Mama ki tafi. Ina so in yi barci.

**Sherifat:** Ban san ki da wannan halin ba, Fati. In dai akwai abin da kika ga zan iya…

**Fati:** E, akwai abin da za ki iya yi! Ki tafi ki ƙyale ni, Mama!

**Sherifat:** Shi ke nan. Shi ke nan, zan ƙyale ki.

**Mai ba da labari:**
A halin da ake ciki kuma, a wani ɓangare na wannan gari, ɗan yaron nan Adams ya shiga wani hali bayan wanda yake ganin kamar cewa kawunsa ne, wato Kawu Jammo, ya ci zarafinshi. Yau mahaifiyarshi ta dafa wani abinci.

**Fitowa ta 4: A gidan su Adams**

**Adams:** Na ƙoshi.

**Precious:** Mene? Adams, ko taɓa abincinka fa ba ka yi ba!

**Adams:** Na ƙoshi.

**Jammo:** Ai yanzu yaron ya girma. Idan ba ya son cin abinci wannan kuma ya rage nashi.

**Precious:** Na sani Jammo, amma wannan irin abincin da ya fi so ke nan. Ina mamaki ya ce ba zai ci ba. Adams, ba wani abu da yake damunka kuwa? Ka tabbata cewa ba za ka ci ba? … Adams! Da kai nake magana!

**Adams:** Zan iya fita waje?

**Precious:** A'a. Ka san na faɗa maka cewa bai kamata kana tashi daga wurin cin abinci ba har sai kowa ya gama.

**Jammo:** Ki bari ya tafi mana idan abin da yake buƙata ke nan. Ki

daina mai da shi ƙaramin yaro mana.

**Precious:** Amma ai ƙaramin yaro ne. Shekarunshi goma kacal. Yaya za a yi ya san abin da ya kamata idan ba a nuna masa ba?

**Jammo:** Adams, kana iya tafiya.

**Adams:** Me?

**Precious:** Wane irin yaro ne wannan! Kana da matsala da kunnuwanka ne? Ka ce kana so ka fita, sannan Jammo, ina nufin Kawu Jammo, ya ce ka tafi.

**Adams:** Wai haka ka ce haka, Kawu Jammo?

**Jammo:** E, Adams. Ka yi abin da kake so. Haka aka san maza.

**Mai gabatarwa:**
A nan kuma za mu ja labulen shiri na yau, sai kuma mun sadu da ku a wani shiri na gaba inda za ku ji abubuwan da za su biyo baya dangane da Hadiza, Fati da Adams, mutane uku da suka fuskanci cin zarafi ta hanyoyi dabam-dabam. Kafin nan kuna iya ziyartar adireshinmu na yanar gizo, wato dw.de/lbe. Ko kuma a buɗe shafinmu na Facebook domin a tattaunawa a kan shirin. Ku huta lafiya.